# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Ni ma ɗan Adam ne: 'Yan Afirkan da ke fama da taɓin hankali
## Kashi na uku: Neman amsoshi


| | |
|---|---|
| Wanda ya rubuta: | Chrispin Mwakideu |
| Wanda ya fassara: | Yusuf Idris |
| Wadda ta tace: | Halima C. Schmaling |


**'Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Duduwa: | 'yar shekara 35 |
| Maude: | ɗan shekara 65 |
| Amina: | 'yar shekara 19 |
| Dije: | 'yar shekara 19 |
| Mudi: | ɗan shekara 50 |

**Mai gabatarwa:**

Jama'a masu sauraronmu, barkanmu da sake kasancewa da ku a kashi na uku na shirinmu na "Ji Ka Karu" wanda muke kawo muku a kan mutane masu taɓin hankali a nahiyarmu ta Afirka. A cikin shirin da ya gabata kun ji yadda ɗalibar nan mai koyon aikin nas ta fara jin surutai kamar aljanu sun kama ta. Wanna ya tsorata ƙawarta da suke zaune a ɗaki ɗaya a makarantar, wato Dije, wanda har ya sa ta fita da gudu domin neman agaji. A can ƙauye kuma, nas Jummai ta ƙi karɓar Duduwa da ɗanta Musa wanda masassara ta kama shi, saboda Jummai ba ta san yadda za ta yi da mai taɓin hankali ba. Sannan shi kuma John wanda ya rasa aikinshi ya ba matarshi mamaki da ya ƙi yarda su tafi wurin ibadarsu, wani abu da bai taɓa yi ba.

Taken shirin namu na yau shi ne "Neman amsoshi". Yamma ta yi sosai a lokacin da Duduwa ta iso wurin mai maganin gargajiyan nan Maude tare da ɗanta Musa.

**Fitowa ta 1: A ƙauye**

**Duduwa:** An gaishe ka, manyan maza! An gaishe ka Maude, mai gani har hanji.

**Maude:** Yauwa! An gaishe ki, Duduwa. Me ke tafe da ke da yaronki?

**Duduwa:** Ba shi da lafiya ne, kuma masassara ce ke damunshi. Kuma ina ganin ciwon kai ma na damunshi. Ko za ka iya ba shi magani domin ya samu sauƙi?

**Maude:** Ba asibiti kuka fara saba zuwa ba idan masassara ta kama ku? Bayan haka ma, na kusa tashi yanzun nan.

**Duduwa:** Yanzu haka ma daga can nake, kuma nas ɗin ta ƙi yarda mu ga likita. Wai ta ce aljanu ne suka kama Musa kuma wai ba su da maganin da za su iya ba shi a can. Shi ne ta ce

wai sai dai mu kai shi babban asibiti a birni inda ƙwararru za su iya duba shi. Koranmu ma dai ta yi daga asibitin, wai Musa yana tsoratar da sauran marasa lafiya. Ni kuma ba ni da kuɗin da zan iya kai shi birni. Shi ne na ce, bari in zo wurinka.

**Maude:** Mmmh, ban san lokacin da mutane za su gane cewa taɓin hankali babbar cuta ce har su riƙa ɗaukanshi da muhimmanci. Shi ke nan, zan ba ki wani jiƙo da za ki ba shi, za ki tafasa ki ba shi a daren nan. Na ga ma ya yi shiru, ina ganin ciwon ya daina damunshi sosai.

**Duduwa:** A'a. Da ma da yamma haka yake yin shiru. Waɗannan mugayen aljanu ne, da rana suka fi damunshi, musamman ma da tsakar rana.

**Maude:** Ina ganin ya kamata ki ƙara kawo min shi wani lokaci, sai in yi magana da aljanun. Ina so in ji dalilin da ya sa suke damun yaronki. Amma yanzu ki karɓi wannan. ... Yauwa. Ki tafasa wannan ganyen sai ki ba shi ruwan ya sha. Zai taimaka wajen warkar da wannan masassaran da ke damunshi. Ki tafi yanzu kuma kar ki waiwayo. Yanzu zan yi sallama da kakannina.

**Duduwa:** Na gode Maude, na gode ƙwarai da gaske. Musa, zo mu tafi gida.

**Mai ba da labari:**

Sai Duduwa da Musa suka kama hanyarsu ta komawa gida, Duduwa na riƙe da ganyayen da Maude ya ba ta a hannu ɗaya, sannan ɗaya hannun kuma tana riƙe da ɗanta. Shin Musa zai samu sauƙi kuwa? Bari mu jira mu gani. Wanshekare a ɗakin cin abinci na makarantar koyon aikin nas, ba wani alamu

da ya nuna cewa Amina ta shiga wani hali, wanda ya sa Dije ta yi ta tunanin cewa wai shin me ya samu Amina ne ran nan.

**Fitowa ta 2: A ɗakin cin abinci a makaranta**

**Amina:** Dije, mene ne? Yaya kike kallona kamar yau kika fara ganina?

**Dije:** Uhm… Ki yi haƙuri Amina. Amma ni ma yanzu ai ban san ma abin da zan ce ba! Ina iya tuna yadda jiya kika ce kina jin wasu muryoyi, kuma ba wasa kike yi ba. Kuma bayan na ruga da gudu neman taimako na dawo, sai kuma kika koma yadda kike kamar wani abu bai faru ba.

**Amina:** Saboda ba abin da ya faru ɗin ne! Saurara ki ji, wataƙila maganar zuciyata ce kawai take fitowa, shi ke nan. Sai kika ji tsoro kika ga kamar na fara hauka ne. Ki yi haƙuri da al'amarin ya sa kika zama kamar ke ce haukan ta kama.

**Dije:** Ba komai. Amma don Allah Amina, kar ki ƙara yi min irin wannan wasan. Idan kika ƙara yi, to gaskiya zan canza ɗakina.

**Amina:** Ke, kar ki damu! Lafiyata ƙalau.

**Dije:** Jira ni zan dawo yanzu, zan ɗan zaga ne.

**Amina:** Bari in zo mu je.

**Dije:** To mu tafi!

**Mai ba da labari:**

Dije na tunanin cewa ba wani abin da yake damun Amina, kuma komai ya zama daidai yanzu. Amma ba a daɗe ba sai ta gane cewa ta yi babban kuskure. Shigarsu banɗakin ke da wuya, sai komai ya ƙara birkicewa.

**Dije:** Amina! Abincinmu zai yi sanyi. Ki yi sauri mu koma. Me kike kallo a cikin madubin ne haka? Har yanzu kina sha'awar kyakkyawar fuskarki ne?

**Amina:** Ke! Wa kike kallo?

**Dije:** Wa nake kallo? Ke nake kallo mana!

**Amina:** Tsaya! Da wa kike magana? Ba na so in ji muryarki!

**Dije:** Ki daina wannan wasan banzan naki! Me kike nufi da ba kya son ki ji muryata? Amina don Allah ki zo mu tafi kafin wasu su zauna mana a wuri.

**Amina:** Na ce ki daina kallona! Ki daina magana da ni! Aaaah! …

**Dije:** Amina! Amina, kin ji wa kanki ciwo. Tsaya, tsaya tukuna! Me yake damunki ne?

**Amina:** Dije, me kika yi? Me ya sa hannuna yake jini? Me ya faru?

**Dije:** Ni ya kamata in riƙa yin irin waɗannan tambayoyin. Amma bari in tsai da jinin tukuna. … Riƙe nan, bari in ɗaure miki in da kika ji ciwon da wannan *hanky* ɗin. ... Ban san abin da ya same ki ba. Yanzun nan kina magana da ni mai daɗi, nan da nan kuma sai kika fara wa kanki ihu a cikin madubi. Amina, kin ga kin tsorata ni da farko. Ba don na san ki ba, da sai in ce kin haukace ne. Amma ina ganin ya

kamata ki ga likitan masu taɓin hankali kafin abin ya wuce misali. Bai kamata ki ci gaba da zama haka ba.

**Amina:** Ni ban san ko mene ne ba. Na kasa yin komai a kai. Ba na ma iya tuna abin da na yi.

**Mai ba da labari:**

Dije ta yi gaskiya. Lokaci ya yi da Amina ya kamata ta nemo amsar abin da ke damunta. Ba halinta ne kaɗai ya canza ba. Tana nuna alamu ma na yin mummunan abu. An yi sa'a shi ƙwararre a kan ƙwaƙwalwa ba shi da nisa da inda suke. Bayan sun kammala cin abinci ba tare da sun ƙara ce wa juna uffan ba, sai suka je don su ga Dr. Mudi. Shi kaɗai ne masani a kan ƙwaƙwalwa a sashen masu taɓin hankali a babban asibitin, wanda mutane kimanin miliyan biyar suke zuwa. Ku ci gaba da sauraro.

**Fitowa ta 3: A asibiti**

**Mudi:** Mara lafiya na gaba! … Yauwa, 'yammata shigo! Yaya sunanki kuma me ke tafe da ke?

**Amina:** To ni dai… ummm… sunana Amina. Kawata Dije na tunanin cewa ciwon hauka na neman ya kama ni, sannan ta shawarce ni da in ga likita. Likitan ƙwaƙwalwa. Tun da kai kaɗai ne a nan, shi ya sa na zo wurinka.

**Mudi:** To tun da ƙawarki tana ganin cewa kina da ciwon taɓin hankali, ke kuma fa? Ke ma kina ganin hakan?

**Amina:** Ban sani ba. Ni ina ganin ba abin da yake damuna.

**Mudi:** Ina duba mutane masu taɓin hankali da kuma waɗanda ba su da isasshen ilimi kullum. Ina tabbatar miki da cewa, wasu da suke ganin cewa ba su da wata matsala a lafiyarsu, sai ki ga sun ma fi waɗanda ake ganin cewa suna da ciwon hauka yin haukan. Amma dai yanzu mu koma kan maganarmu. Ke ɗalibar koyon aikin nas ce?

**Amina:** Na'am, ee! Yaya aka yi ka gane? Kana ma iya karanta zuciyata ce?

**Mudi:** Hehehe, ƙwarai da gaske! Me kike zato? Ni fa likitan ƙwaƙwalwa ne! Amma dai mu aje wasa a gefe ɗaya, ba zan iya karanta zuciyarki ba. To, amma rigar da kika sa ta masu koyon aikin nas ce, sannan kuma duk wanda ya daure miki hannun nan da kika ji ciwo ƙwararre ne, kuma ina ganin ɗaya daga cikin waɗanda kuke karatu ne ta yi miki. Me ya same ki a hannun? Ko kin ji wa kanki ciwo ne da rezar da kuke aiki da ita?

**Amina:** A'a likita. Wannan shi ne ma abin da ya fi ba ni tsoro. Ina ganin ni na ji wa kaina ciwo, amma dai ba da gangan ba. Sai dai lokacin da na shiga irin halin ruɗewa. Ta yaya zan yi maka bayani ma? Ba na ma iya tuna abin da na yi. Amma Dije, ƙawata a makaranta, ta ce wai na je banɗaki ne sai na fara yi wa kaina ihu bayan na kalli kaina a madubi. Sannan kuma sai na bugi madubin, na fasa shi, kuma na ji wa kaina ciwo.

**Mudi:** Ko kin san abin da ya sa kika yi hakan?

**Amina:** Ina ganin kamar ina tunanin za a cutar da ni ne. Amina ta ce wai ina jin maganganu ne da ita ba ta ji. Haka na iya faruwa? Me yake damuna?

**Mudi:** Amina, ina ganin ya kamata ki riƙa zuwa wurina a kai-a kai. Zan so in san sahihin abin da yake damunki. Daga abin da kika faɗa min yanzu, yana iya yiwuwar cewa kina da matsalar ƙwaƙwalwa.

**Amina:** Ni? Matsalar ƙwaƙwalwa?

**Mudi:** Kwarai kuwa! Amma kada ki tsorata. A yanzu ba zan iya tabbatarwa ba. Amma ana ɗaukar lokaci kafin a gane cewa mutum yana da ciwon ƙwaƙwalwa, ba a gudanar da wani gwaji ko wani abu makamantan hakan. Ba dai a ƙasarmu ba. Amma zan tabbatar miki da cewa, idan har kina samun magunguna da kyakkyawar kulawa, za ki samu lafiya kuma ki ci gaba da rayuwarki. To tun da yanzu zan je in duba marasa lafiya, ina ganin ya kamata ki bari sai gobe ki dawo.

**Amina:** Na gode likita. Amma ba ka ganin cewa ina iya ciwon hauka ko?

**Mudi:** A'a. Ke mara lafiyata ce. Ni kuma ba na kiran waɗanda nake kula da su mahaukata.

**Mai gabatarwa:**

Da wannan tabbaci na Dr. Mudi muka kawo ƙarshen wannan shiri na yau. Shin Dr. Mudi, wanda shi ne kaɗai likitan ƙwaƙwalwa a garin zai iya taimakon Amina kuwa? Shin Musa zai samu lafiya kuwa har ya riƙa yin rayuwa kamar sauran jama'a? Sannan ya John, kuma wanda shi ma ya shiga halin ciwon takaici? Ku kasance da mu a shiri na gaba domin jin yadda za ta kaya. Kafin nan kuna iya ziyartar adireshinmu na yanar gizo domin sake sauraron wannan shirin. Adireshin namu shi ne dw.de/lbe. Kazalika kuna iya ziyartar

shafinmu na Facebook don tattaunawa a kan shirin. Sai mun sadu a shiri na gaba. Ku huta lafiya.